# Littafi mai Tsarki na yara
## Ke gabatar da

# Allah ya gwada kaunar Ibrahim




Wanda ya Rubuta: Edward Hughes

Mai Zane: Byron Unger; Lazarus
Alastair Paterson

Mai niyyan daukan nauyi: M. Maillot; Tammy S.

Fassarawa: Bible Society Nigeria

Wanda ya Wallafa: Bible for Children
www.M1914.org



©2024 Bible for Children, Inc.
Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan
har ba zaku sayar da shi.






Wata rana da daddare sai Allah ya ba wa Ibrahim wani umarni mai wuyan ganewa. Gwaji ne domin a gane ko Ibrahim yana son yaronsa Ishaku fiye da Allah.


"Dauki danka Ishaku, sai ka mika shi hadayar konawa," Allah ya umarta. A mika Ishaku hadaya? Ya mika dansa hadaya? Abu mai wuya ne ga Ibrahim. Yana kaunar dansa sosai.
3


Amma Ibrahim ya riga ya amince da Allah duk da rashin fahimtar komen da ke faruwa. Da sassafe sai ya kama hanya zuwa tuddun hadayan tare da Ishaku da masu hidimarsa biyu.
4


Kafin ya kama hanya, Ibrahim ya faffashe itacen hadayar konawan. Ibrahim ya shirya ya yi wa Allah biyayya.
5


Bayan kwana uku sai suka yi kusa da tuddun. "Ku tsaya a nan," Ibrahim ya gaya wa masu yi masa hidima. "Za mu je mu yi sujada, sa'an nan mu dawo gareku." Ishaku ya dauki itacen;
Ibrahim yana rike da wuta – da wuka.
6


"Ina dan tunkiya na hadayar?" Ishaku ya tambaya. "Allah zai tanada dan tunkiyar da Kansa," Ibrahim ya amsa.
7


Su biyu suka zo daidai wurin da Allah ya zaba. A wurin, Ibrahim ya gina bagadi ya kuma shirya itacen don kona hadaya a gaban Allah. Ibrahim ya gina bagadai dayawa. Babu shakka wannan ya zama mai wuya fiye da sauran.
8


Ibrahim ya daure Ishaku, ya daura kaunataccen dansa din a kan bagadin. Da gaske ne Ibrahim zai yi biyayya ga Allah har ya mika kaunataccen dansa Ishaku makadaici hadaya?
9


I'i! Sai bakin wukan yana walkiya yayinda Ibrahim ya daga shi sama. Babu shakka zuciyarsa yana ta karaiya, amma Ibrahim ya sani cewa dole ne ya yi biyayya ga Allah.
10


"TSAYA!" Mala'ikan UBANGIJI ya yi ihu. "Yanzu na sani kana tsoron Allah. Ba ka hana da danka, makadaicin danka, daga gareni ba."
11


Da ganin rago a wani dan daji, sai Ibrahim ya kunce Ishaku sai ya mika ragon hadaya maimako Ishaku. Watakila Ishaku yana tunani cewa "Ko Allah ya tanada kamar yadda Babana ya fada ne."
12


Sa'ad da uba da dansa suna sujada, Mala'ikan UBANGIJI ya yi magana da Ibrahim. "A cikin 'ya'yanka, duka al'ummai za su sami albarka saboda ka yi biyayya." Wata rana, za a haifi Yesu ta wurin zuriyar Ibrahim.
13


Ibrahim da Ishaku suka koma gida. Bayan dan lokaci, bakin ciki ya same su. Saratu ta mutu. Ibrahim ya rasa matarsa, kuma Ishaku ya rasa mahaifiyarsa.
14

Bayan jana'izar, sai
Ibrahim ya aiki shugaban
'yan hidimarsa don ya nema
wa Ishaku mata. Sai dan hidimar ya
tafi garin Ibrahim domin ya nema masa mata
daga dangin Ibrahim.



15

Dan hidimar ya roki Allah ya nuna masa wata alama. "Bari yarinyar da za ta ba rakumaina ruwa ta zama wadda ta dace ga Ishaku." Nan da nan sai Rebekka ta yarda ta ba su ruwa. Ita daya ce daga cikin dangin Ibrahim. Sai dan hidimar ya gane cewa Allah ya amsa addu'arsa.



16

Rebekka ta bar iyalinta domin ta aure Ishaku. Sai ta yi masa ta'aziya bayan da mahaifiyarsa ta mutu. Ishaku ya nuna mata kauna babu iyaka.



17

**Allah ya gwada kaunar Ibrahim**

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Farawa 22-24**

**"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130**

18




5 60

19

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:
Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**

20